


# A DAINA KASHE-KASHE!

## KU ZO, MU YI TUNANI

Kai matashi da ke matashiya ku zo-ku zo, mu yi tanani, mu yi tunani tare. Shin kashe-kashen da ake a wannan kasa bai yi yawa ba? Shan jinin da ake bai yi yawa ba? A jihohin Nassarawa, Taraba, Benue, Bauchi, Plateau da Borno, 'yan Nigeria na kisan junansu. Jama'a na mutuwa a kullum-dubbai a nan, daruruwa a can. Ana kona gidaje, mata da yara babu gidajen zama, ana kisan mazajensu. Ana halaka Hausawa, da Ibo da Yarabawa, da Edo da Tiv, a Masallatai da Majami'oi, a makarantu, kasuwanni da kan Tituna. Babu tsaro a ko ina, jama'a na halaka a ko ina. Wannan hali kuke so a kasarku, a garunku da gidajenku?



Wadanda suke saka kashe-kashennan, da saka boma-boman nan da harbe-harben nan, basa yi da kansu ko su turo 'ya'yansu. Face suna turo 'yan'yan talakawa da 'yan Nigeria marassa galihu-suna amfani da matasa maza da mata kamar ka/ki. Suna amfani da matasa masu yunwa a jiki, masu saurin fushi domin rashin aikin yi, duk da cewa suna ta nema sun rasa; masu saurin fushi domin suna kallo masu dukiya na ta samun kari da yin kiba; masu saurin fushi domin talauci na

karuwa akan talaka kuma talakawa na kara ramewa.
Amma an manta da cewa kisan talakawa da sauran masu yunwa a jika ba shine mafita ba. A gaskiya mutanen da suke hayarka domin kashe 'yanuwanka sune babbar matsalarmu. Sune suke kawo talauci da wahala a cikin kasa, domin sune suke sace kudin al'ummar kasa. Saboda haka, don me zaka bata kan ka da rayuwarka domin biyan bukatunsu?

Ke matashiya, kai matashi ku zo-ku zo, muyi tunani. Matasa na cikin fushi domin basu da ayyukan yi. Shin kun san hukuma na tanade-tanaden bamu ayyukan yi? Akwai shirye-shiryen hukuma don bamu ayyukan yi tare da bamu bashi domin yin kasuwanci. Amma bama jin ina aka tsaya, bama samun ayyukan yi ballantana bashin. Menene dalili? Domin hukuma bata shawartarmu akan shirye-shiryenta garemu, kuma ba'a saka mu a cikin yadda ake tafiyar dasu. Basa sanar damu akan shirye-shiryen da hukuma ke yi; a lokacin da zamu sani tuni sun riga sun rabawa 'ya'yansu da yayan abokansu. Ku kuma fa? Kuna ci gaba da zama a cikin rashin aikin yi, domin 'yan siyasa suna hayar ku domin kisan yan-uwanku 'yan Nigeria.

Lokaci ya yi da za'a daina wannan. Duk matasa marassa ayyukan yi su hadu, su ki yin amfani da su don tashin hankali da kashe-kashe. Matasa su bukaci cewa a sanar da kowa shirye-shiryen samar da ayyukan yi a Gwamnatin tarayya, da Gwamnatin jiha a kananan hukumomi don duk matasa marassa ayyukan yi su sadu da amfanin shirye-shiryen da hukumomi keyi domin su.
Ta yaya matasa zasu san shirye-shiryen da hukumomi suke tunani? Ka/ki neme mu a Cibiyar Hakkin Yan Adam da Wayar da Kai ko adireshin layinmu, ko ta adireshin yanar gizo, ko lambar wayar mu kamar haka.

**A DAINA KASHE-KASHE! A SHIGO CIKIN GWAGWARMAYA!!**

**Daga: Cibiyar Hakkin 'Yan Adam da Wayar da Kai,** dake kantin Sheshe hawa na Karshe, Fuloti mai Lambar 6/7 akan Titin Hadejia Unguwar Yankaba Kano,
Lambar Waya 08099260514, 08023133924 ko kuma 08034130114, ko kuma yanar gizo kamar haka chcenigeria@yahoo.com

Tare da tallafin Offishin Kasa da Kasa mai Shirye-Sheiryen Karfafa Zaman Lafiya a Nigeria (NSRP)

CHRICED

nsrp
NIGERIA STABILITY AND RECONCILIATION PROGRAMME